*Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 012 (Pg. 131-143)*

**Bukin Sallar Gani Jiya da Yau: Nazari Daga Wasu Masarautun Kasar Hausa**

**Dr Ginsau Abdulkadir**
abdulkadirgins2017@gmail.com
*0803 237 7941, 0705 282 0708*
Sashen Harsunan Nijeriya da Kimiyyar Harshe
Jami'ar Sule Lamiɗo Kafin-Hausa
Jihar Jigawa

**Dr Yahuza Usman Musa**
yahuzausmanmusa@gmail.com
*08037329263*
Sashen Harsuna da Kimiyya
Jami'ar Jihar Taraba, Jlingo
Jihar Taraba

***Tsakure***

*Wannan taakarda ta yi ƙoƙarin binciko tare da bayyana yadda bikin sallar gani ya samo asali da masarautun da suke gudanar da shi, sannan da yadda ake aiwatar da shi, da cakuɗuwarsa da bikin maulidi, da bayyana tasirin zamani a kansa. Domin haka aka bibiyi ayyukan magabata waɗanda suka yi tsokaci ko sharhi game da bikin da kuma kai ziyara gani d ido masarautu lokacin gudanar da bikin sannan kuma aka yi hira da mahaya da mahalarta taron bikin a masarautar Haɗejiya da Daura da Gumel da kuma Damagaram da ke Jumhuriyar Nijar. Saboda haka binciken ya gano abubuwa masu tarin yawa dangane da samuwar asalin bikin; ya samo asali ne tun daga tsohuwar dalar Borno. Ya samu ne ta dalilin sarakunan Hausa bakwai na daular Daura. Ana gudanar da al'adu iri daban-daban lokacin bikin, wasanni da kaɗe-kaɗe da raye-raye da hawan dawaki cikin shigar yaƙi da ƙawa da sada zumuncin 'yan uwa da cinikayyar kayayyakin gargajiyar Hausa da samin ziyarar baƙi masu maƙwabtaka da Hausa da tasirin zamani a kansa.*

***Keɓaɓɓun Kalmomi:*** *Biki da gani da masarautu da jiya da yau.*

## 1.1 Gabatarwa

Bukin sallar gani, buki ne da ya samo asali tun lokaci mai tsawo, ana gudanar da shi a tsohuwar daular Borno ta El-Kanemi. Hausawa suna gudanar da shi a farko ko ƙarshen shekara, musamman lokacin kaka yayin da ruwan sama ya ɗauke aka yanke albarkatun gona. A wannan lokaci kowa ya cika rumbunsa da kayan abinci, an ci, an sha, an ƙoshi, an yi ƙiba ɓul-ɓul, babu abin da ake da buƙata sai nishaɗi da annashuwa. Wannan ya sa suke yin buki domin nuna farin ciki da godiya da murnar zagayowar shekara, sannan da nuna al'adunsu na gargajiya ta hanyar nishaɗantar da junansu. A wannan lokaci ne masu sana'a ke nuna bajinta wajen nuna fasaha ko yin wani siddabaru da ya jiɓanci sana'arsu.

Ana haka sai shugabanci ya shiga lamarin, ake ware ranakun gudanar da bukin da kuma irin wasannin da ake gudanarwa a kowace rana. Da haka ne ya gangaro har ya zama

masu iko na sarauta sun karɓe bukin, wajen ganawa da ʻyan uwansu na nesa, musamman sarakunan ƙasar Hausa bakwai (Daura), domin tattauna al'amuran mulki. Sannan suka ƙawata shi da hawan ingarmun dawaki da nuna kayayyakin yaƙi, da kai ziyara ga ʻyan uwansu mata, domin nuna musu ƙauna da girmamawa.

Ana wannan hali da al'ada, addinin musulunci ya shigo ƙasar Hausa, har aka sami ƙarin bukukuwa da suka shafi addinin na musulunci. A cikin bukukuwan musulunci, akwai bukin maulidi na ranar tunawa da haihuwar fiyayyen halitta, wato Annabi Muhammad, tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi. Wanda mafi akasari yakan zo ne a ƙarshen zamani lokacin kaka. Wannan ta sa Sarakunan wancan zamani suka mayar da ranar bukin gani ta zo daidai da wannan rana ta maulidi, domin a gudanar da shagulgulan bukin gani da maulidi lokaci guda. Saboda haka suka faɗaɗa kai ziyara ga tsangayun malaman addini, domin taya su murnar zagayowar wannan rana.

Wannan buki na gani yana da matuƙar tasiri a wajen masu gudanar da shi, domin akan ƙulla alaƙa tsakanin maza da mata har a yi aure, wani lokaci kuma a sami saki (idan saɓani ya afku). Sannan a lokacin bukin akan sami ziyarce-ziyarce da bayar da kyaututtuka ga ʻyan uwa da abokan arziƙi da gudanar da al'adu masu tarin yawa. A fannin cinikayya kuwa, tattalin arziƙin Hausawa kan haɓaka a dalilin wannan buki. Haka kuma, akan sami shigowar baƙi daga garuruwa da ƙasashe masu maƙwabtaka da Hausa, domin ƙulla alaƙa da sarakunan waɗannan masarautu da kuma yin cinikayyar kayayyakin gargajiyar Hausa.

Domin haka wannan takarda ta yi tsokaci ne game da asali da yadda ake gudanar da bukin sallar gani, da kuma fito da wasu muhimman al'adun Hausa da ake gudanarwa a lokacin bukin a masarautun Daura da Haɗejiya da Gumel da kuma Damagaram. Yin hakan yana da matuƙar muhimmanci ga manazarta al'adun Hausa da adabi da kuma wani fanni na tarihin Hausawa da maƙwabtansu.

### 1.2 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce:

- tantance asalin samuwar bukin sallar gani a ƙasar Hausa, domin nuna masarautun da suka fi ba shi muhimmanci da kuma tasirin da yake da shi gare su.
- gwada yadda masarautu ke gudanar da bukin sallar gani a jiya da kuma yau.
- fito da muhimman al'adun gargajiyar Hausa da ake gudanarwa lokacin bukin.
- fayyace alaƙar bukin sallar gani da bukin maulidi.

### 1.3 Hasashen Bincike

Wannan bincike yana hasashen cewa:

1. dalilin samuwar bukin sallar gani da al'adun da ake gudanarwa a ciki sun banbanta daga masarauta zuwa masarauta. Ko wannan yana nuna tasirin zaman wasu masarautu a ƙarƙashin daular Borno da wasu daga masarautun Hausa bakwai.

2. akwai alaƙa mai ƙarfi tsakanin masarautun da ke gudanar da wannan buki na sallar gani duba da kusanci ko maƙwabtakar ƙasa da ƙabila da al'adu iri guda, da kuma hulɗar aurataiyya da kasuwanci da ke tsakaninsu da juna.
3. al'adun da sarakuna da jama'ar gari ke gudanarwa a lokacin bukin sallar gani su na ƙara bayyana kyawawan al'adun Hausa, sannnan da fito da ɗaga daraja da martabar Hausawa a idon al'ummun duniya.
4. bukin sallar gani fuska biyu gare shi, addini da al'ada, domin wasu na danganta shi da addini kai tsaye, yayin da wasu ke ɗaukansa a matsayin al'ada zalla.
5. ratsowar da bukin sallar gani ya yi cikin zamunna, ya kawo an sami sauye-sauye da dama wajen yadda ake gudanar al'adu a bukin tun asali, wato da alamun zamani ya yi tasiri a kansa.

### 1.4 Farfajiyar Bincike

Wannan bincike ana gudanar da shi ne a kan wani ɓangare na al'ada, al'adar da ake dubi kuma ita ce fannin bukukuwan Hausa. Saboda haka aka taƙaita a bukin sallar gani, domin ya zame mana garkuwar aiki, sannan kuma an taƙaita ne a masarautu huɗu kawai (Daura da Haɗejiya da Gumel da kuma Damagaram) domin kusan su suka fi ba wannan buki muhimmancin gaske fiye da wasunsu.

### 2.1 Buki

Masana da manazarta al'ada da adabi sun yi iya bakin ƙoƙari wajen tofa albarkacin bakinsu game da asali da ma'anar buki da kuma yadda Bahaushe ke kallonsa ta fuskoki da dama. Buki wani abu ne da ke cikin tsofaffin al'adun mutanen da, da wuya a tantance ranar da aka fara shi. A duniyar da muke ciki yau, babu al'ummar da ba ta da buki, kuma babu al'ummar da ta yi watsi da bukukuwan da ta gada kaka da kakanni. Saboda haka, a al'adance, gidan kowa ana buki, garin kowa ana buki, ƙasar kowa ana buki, a addinin kowa akwai buki, a matakan rayuwar kowa akwai buki. Samun taron mutane a buki bai da makawa kamar yadda hidimomi da hada-hada cikin kowane buki ya zama suturar ƙawa ga bukin. Kamar yadda Funtua da Gusau (2010) suka nuna cewa, buki al'ada ce da kowace al'umma ta duniya take yi a wasu lokuta na musamman, bisa manufar nuna farin ciki da faruwar wani muhimmin al'amari da ya sami wani ko wasu daga cikin al'umma.

Kamusun Hausa (2006) an bayyana buki da cewa, shagali ne na nuna farin ciki wajen aure, ko suna, ko naɗin sarauta, ko salla, ko al'adun gargajiya. Sai Tsanyawa (1983) ya ce, buki a Hausance yana nufin taruwar al'umma/jama'a domin nuna farin cikinsu tare da shagali game da wani abu da ya faru. Domin haka muna iya cewa buki shi ne duk wani abu taron shagali da akan yi, ko dai domin nishaɗi ko domin nuna murnar samun wani abu ko kuma a lokacin da ake gudanar da wani aiki. Galibi akan ba da goron gayyata bayan an sa lokaci. Yahaya da wasu (1992) sun yi bayani a kan fannin da ya shafi bukukuwa a ƙasar Hausa, wanda suke aiwatarwa kamar yadda ko wacce al'umma take yin bukinta tare da yin al'adu a cikin bukin, wanda suka gada tun iyaye da kakanni. Da kuma wasu al'adunsu da suka

samo tushe da asali tun ran gini, ran zane. Wasu al'adun suna tattare da bukukuwa da ake aiwatarwa sannan kuma sun kawo nau'o'in irin bukukuwan da ake a ƙasar Hausa, wanda daga ciki har da bukin maulidi wato bukin gani, wanda ake yi domin tunawa da ranar da aka haifi shugabanmu Annabi Muhammadu, tsira da aminci su tabbata a gareshi. Akan yi wannan buki a daren ko ranar (12) ga watan Rabi'ul Auwal na shekarar Musulunci.

### 2.1.2 Bukin Gargajiya:

Wannan yana nufin duk wasu bukukuwan da Hausawa suke gudanarwa dangane da irin tsarin al'ada ta rayuwar Bahaushe, su bukukuwan na gargajiya ba su da alaƙa ko dangantaka da tsarin addinin musulunci. Watau dai gargajiya ce tsantsa. Saboda haka, bukukuwan Hausawa na gargajiya su ne irin su bukin shan kabewa da suka yi masu 'yan canje-canje suka mayar da su kamar bukukuwansu na gargajiya. Irin waɗannan bukukuwa sun haɗa da bukin sallar idi da bukin Maulidi da bukin sallar cika-ciki da bukin sauƙar Alƙur'ani (Ibrahim, 1982:256).

### 2.1.3 Bukin Addini

Bukin addini kuma, shi ne duk wani bukin da Hausawa suke gudanar da shi, waɗanda a zahiri za a samu wani tasiri na addini tun kafin gudanar da bukin da lokacin da ake aiwatar da shi. A irin wannan buki na addini ba wai ana nufin sam babu wani abu da ya shafi al'adar gargajiya ba, ana samun ta kace-kace a ciki, amma dai maganar addinin ta fi ƙarfi ko tasiri a cikin bukin. Misali: bukin Takutaha da bukin salla babba da ƙarama da sauransu.

A aikin Gwarzo, (2005) kuwa an raba buki zuwa gida uku ne kamar haka:

1. Buki na yanayi (damina ko rani ko hunturu ko rana ko yammaci ko dare da sauran su)
2. Buki na lokaci (bukin sallar gani)
3. Buki na kurum (naɗin sarauta ko daba da makamntansu)

Bukukuwan Hausawa rukuni biyu ne kamar haka:

1. Wanda yakan faru lokacin da aka sami ƙaruwa, kamar bukin aure ko haihuwa (suna).
2. Bukin da yakan shafi al'ummar gari baki ɗaya, kamar bukin kalankuwa da na salla da dai sauransu (Funtua da Gusau, 2010:1 da Fatima, 2018:15).

Shi kuwa Magaji (2002) cewa ya yi, a farfajiyar nazarin al'adar buki a ƙasar Hausa, matakan bukukuwa su ne: Bukukuwan matakan rayuwa da tsari da yaƙi da buɗi da dattako da naɗi da dubu da tambarci da ban gaskiya da sauƙaƙƙin addinai da tsafe-tsafe da siddabaru da sana'o'i da kafa tubalan harsashe da askewa (tuba) da kuma bukukuwan gayya.

### 2.2 Wasu Bukukuwan da Musulunci Ya Zo da Su

Kafin zuwan Musulunci ƙasar Hausa, Hausawa suna da bukukuwansu da suke gudanarwa lokaci-lokaci waɗanda suka jiɓinci harkokin rayuwarsu imma a al'adance ko kuma a addininsu na gargajiya. Bayan zuwan Musulunci ne kuma, sai aka sake samun ƙarin wasu bukukuwa waɗanda

suka shafi musulunci kai tsaye, daga bisani kuma aka sami gaurayen addini da al'ada a bukukuwa. Domin haka akwai bukukuwa masu nuni da al'ada tsantsa kamar kalankuwa da gauta da naɗin sarauta da sauransu, sai kuma masu raɓi da addinin musulunci ko na gargajiya kamar babba da ƙaramar salla da cika-ciki da takutaha da shara da buɗar dawa da shan kabewa da makamantansu. wannan yay i daidai da ƙaulin Bello, (2008:8) da yake cewa, bukukuwan da addinin Masulunci ya zo da su ƙasar Hausa sun haɗa da; sauƙar karatun Alƙur'ani mai girma da bukin sallar idi babba da ƙarama da bukin Maulidi na murnar zagayowar ranar da aka haifi fiyayyen halitta da Takutaha da dai sauran bukukuwa masu alaƙa da addinin na Musulunci da dama.

### 2.3 Masarautun da ke Gudanar da Bukin Sallar Gani a Yau

Masarautun da ke gudanar da bukin sallar gani a yau suna da yawa sai dai a ce waɗanda suka fi ba shi muhimmanci, da kuma waɗanda aka zaɓa domin yin nazari. Saboda haka masarautun su ne; Masarauatar Daura da Haɗejiya da Gumel da kuma Damagaram da ke jumhuriyar Nijar. Dukkan waɗannan masarautu suna cikin ƙasar Hausa ne kuma bisa ga tarihin samuwa ko zaman mulki duk sarakunansu sun zauna a ƙarƙashin daular Borno tun lokacin El-Kanemi, duk da cewa a yau suna bin daular Usmaniyya ta Sakkwato ne in banda masarauatar Damagaram da ke jumhuriyar Nijar mai cin gashin kanta, domin ita ma Sultan gareta kamar Sakkwato.

A fannin ƙasa, masarautun a ɗamfare suke da juna, domin sun yi iyaka da juna ta fuskoki da dama, koda kuwa akwai tazarar gari, to, sai dai bisa tsarin taswirar iyakar gwamnati. Saboda haka, a yau masarautar Daura tana jihar Katsina ne, daga gabas da arewa ta yi iyaka da wasu ƙauyukan Jumhuriyar Nijar (Damagaram), daga kudu ta yi iyaka da masarautar Kazaure, sannan daga yamma ta yi iyaka da masarautar Katsina.

Masarautar Haɗejiya kuwa kamar yadda Wakili, (1989:1) ya ce, Haɗejiya daɗaɗɗiyar masarauta ce, tana ɗaya daga cikin masarautu waɗanda suka yi fice a masarautun tsohuwar daular masu jihadi ta Sakkwato. Sunan masarautar ya samu ne daga babban birnin masarautar wato Haɗejiya. Daga lokacin kafuwarta kawo yanzu, masarautar ta yi fice da yin suna bisa ga muhimman tarihi da take da shi. Masarautar Haɗejiya tana daga cikin masarautun da sarakunan Haɓe suka mulka kafin jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo. Haɗejiya tana arewa maso-gabas tsakanin daular Borno da ta Sakkwato (Abbas, 2017:1,20). A ƙarni na sha tara (ƙ19) ta kasance ƙaramar masarauta amma kuma mai ƙarfin dakarun yaƙi a gabashin daular Sakkwato. Masarautar tana gabas daga arewa ta yi iyaka da masarautar Gumel, daga arewa maso gabas ta yi iyaka da masarautar Bade dake jihar Yobe, daga kudu ta yi iyaka da Katagum da ke jihar Bauchi, sannan daga yamma kuma ta yi iyaka da masarautar Ringim da Dutse da ke jihaar Jigawa.

Maigatari (2015:16) da Saifullahi (2019:30) sun yi tarayya yayin tattauna asalin kafuwar garin Gumel da bayar da tarihin masarautar. Suka ce, tarihin masarautar Lautai (Gumel) ya samo ne daga birnin Ngazargamu wanda

ke ƙarƙashin daular Fikeami ta Borno. Waɗanda suka samar da asalin masarautar Mangawa ne. Masarautar Gumel tana ƙarƙashin mulkin Borno ne, har lokacin zuwan Turawa, hatta naɗin sarakunan Gumel a ƙasar Borno ake yi a fadar Maiko Shehu (Sayfullahi, 2019:32). Mafi rinjayan masarautar Gumel daga arewa da kuma kudu maso yamma ta yi iyaka da jumhuriyar Nijar (Damagaram). Yayin kuma daga kudu maso-gabas ta yi iyaka da ƙasar Machina da ke jihar Yobe. Daga gabas maso kudu ta yi iyaka da masaautar Haɗejiya, sai kuma daga wani ɓangare a arewa da yamma ta yi iyaka da masarautar Ringim.

Tarihin masarautar Damagaram ba zai cika ba har sai an dangana ga tsohuwar daular Borno ta El-Kanemi, domin daga can ne tushen su ya samo asali. Haka kuma sai an taɓo magana a kan Daura, saboda kusancin masarauta da taimakon juna da aka samu a tsakani ta fannonin maƙwabtaka da auratayya da shugabanci da kasuwanci da sauran hanyoyin gudanar da rayuwa da dama. Damagaram tana kan babbar hanyar zuwa cikin jumhuriyar Nijar daga gabas maso yamma da arewa maso kudu zuwa Agadaz zuwa Kano a Nijeriya.

### 3.1 Bukin Gani

Bukin sallar gani, buki ne da yake da daɗaɗɗen tarihi cikin tarihin ƙasar Hausa, sai dai binciken ya fahimci akwai ra'ayoyi mabanbanta tsakanin masu gudanar da bukin, wajen furucin kalmar ta 'gani' da bayyana ma'anarta. Saboda haka wasu ke ganin asalin kalmar gani ta samo asali ne daga '**Gaanii**' mai nufin ganawa wato zantawa da juna a mabanbantan ra'ayi da fahimtar magabata (Lange, 2012:245 da hira da Alh. Bashir Daura). Wasu kuma suka ce, kalmar tana nufin '**ga ni**' mai nufin "ga ni, na zo, mu gana/ga ni na zo gida" kamar yadda wasu magabatan suka tafi da wannna ra'ayi. Wannan ya yi daidai da fahimtar Mayaƙi Gumel (2019), da ya ke bayar da tasa fassarar sai ya ce, kalmar gani tana nufin /**ga'in/,** wato gani mu gana/zo mu gana da juna.

#### 3.1.1 Samuwar Bukin Sallar Gani

Binciken ya tattauna dangane da asali ko samuwar bukin sallar gani a ƙasar Hausa, saboda haka binciken ya sami ra'ayoyi mabanbanta juna dangane da gari ko masarautar da ta fara gudanar da bukin. Wasu na alaƙanta samuwar bukin da al'adun ƙabilun gabashin duniya waɗanda suka yiwo ƙaura zuwa ƙasar Hausa ta yau, har suke kafa hujja da irin wasan bori da ake gudanarwa a ƙasar Hausa da wasan wuta (babule/wowo) wadda ya yi daidai da wasan wutar da Parisawa ke yi a matsayin bauta.

Wasu kuma na ganin bukin ya samo asali ne daga Daura, ta dalilin 'ya'ya da jikokin Bayajidda waɗanda ke riƙe da masarautun Hausa bakwai, domin haka suke taruwa a Daura su gana da juna da nufin:

1. Murnar shigar jarumi Bayajidda cikin masarautar Daura, afkuwar al'amuran da suka faru ya haifar da bukukuwa na murna.
2. Murnar rabuwa da musifa (Maciji Sarki).
3. Murnar samin sabon jagora, kuma jarumi a matsayin Sarki.
4. Murnar samin alaƙar auratayya da ta ƙullu tsakanin Bayajidda da Sarauniya (Lange, 2012).

Akwai kuma ƙaulin da ke cewa, bukin ya samo asali ne daga tsohuwar daular El-Kanemi ta Borno, domin a can ake gudanar da shi. Shehun Borno shi ke tara sarakunan yankinsa duk shekara ya gana da su, ya karɓi koken kowane sarki da talakawansa, sannan ya yi musu jawabi. A wannan lokaci yakan iya sauƙe duk sarkin da aka samu da wani laifi, sannan a naɗa wani sabo. Daga nan kuma sai a ƙayatar bukin da hawan dawakai, domin nuna nagartattun dawakai da kayan yaƙi da kuma samin nishaɗi. Wannan ya yi daidai da da'awar mutanen Gumel da ke cewa, a ƙasar Hausa bukin ya samo asali ne daga masarautar Gumel, tun zamanin da masarautar ke ƙarƙashin daular Bornu, (Gumel, 2019).

Haka kuma an gano akwai masu da'awar bukin sallar gani a ƙasar Hausa ya wanzu a masarautar Haɗejiya, lokacin masarautar Daura da Gumel da Kazaure suna ƙarƙashin Rasdan guda, lokacin da Turawan mulkin mallaka ke gudanar da ikonsu a ƙasar Hausa kafin a sami 'yancin kai. A wancan lokacin shalkwatar Turawa tana Haɗejiya ne, domin haka kowane sarki nan yake zuwa domin jaddada mubaya'arsa da gaisuwa ga Bature. (Wakili, 2005:16)

### 3.1.3 Bukin Sallar Gani Kafin Zuwan Musulunci Kasar Hausa

Bincike ya gano bukin sallar gani kafin zuwan Musulunci ƙasar Hausa, a mafi rinjayen zance, ya samo asali ne daga tsohuwar daular Borno da kuma 'ya'ya da jikokin Bayajidda waɗanda ke riƙe da sarautar manyan masarautun ƙasar Hausa, wato waɗanda ake kira da Hausa bakwai (Lange, 201:141). Domin binciken ya gano cewa, tarihi ya nuna suna gudanar da bukin ne bisa tsarin addinin gargajiya a duk shekara. Wannan kuwa ya tabbata a tarihin Bagauda na Kano, da kuma tarihin Tsumburbura, kamar yadda Dokaji, (1978:7) ya bayyana.

### 3.1.4 Bukin Gani Bayan Zuwan Musulunci Kasar Hausa

Zuwan Musulunci ƙasar Hausa ya zo da sauye-sauye a ɓangarori da dama waɗanda suka shafi addini da al'adu da sauran al'amuran zamantakewar yau da kullum. Saboda haka binciken ya fahimci bukin gani yana ɗaya daga cikin waɗanda suka sami sauyin yadda ake gudanar da shi, da irin manufofin da suka sa ake aiwatar da shi. A can zamani mai tsawo, ana gudanar da bukin gani ne domin nuna murnar zagayowar shekara, wanda ake gudanarwa a farkon shekara musamman lokacin kaka bayan ɗaukewar ruwan sama, amfanin gona ya iso gida. A wancan lokaci ana gudanar da bukin ne da yin wasanni da wasu al'amura na bautar gargajiya, wanda daga bisani ya rikiɗe zuwa al'adun al'umma na ganawa da juna saboda sauyin wurin zama. Sannan kuma sai ya koma hannun masu mulki, yayin da suke gudanar da shi da nufin ganawa da junansu domin sada zumunci da tattauna harkokin mulki da kuma ba da shawarwari yadda za a inganta zamantakewar al'ummar masarauta.

Daga cikin mabiya addinin Musulunci musamman ɗariƙun sufaye, sun zo da bukin murnar zagayowar fiyayyen halitta Annabi Muhammad (tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gareshi), wanda suke gudanar da shi a watan uku a tsarin kalandar Musulunci, wato ranar sha biyu ga watan Rabi'ul Auwal. Bukin yakan zo daidai da lokacin da

ake gudanar da bukin gani, wannan ya sa aka haɗe shi rana guda domin a riƙa gudanar da bukukuwan a lokaci guda. Saboda haka sai bukin ya ɗauki sabon salo wajen manufar da ta sa ake gudanar da shi, da kuma irin al'adun da ake gudanarwa a lokacin, maimakon al'ada zalla sai aka gwama shi da wasu al'amura na addinin Musulunci. Domin haka binciken ya gano a masarautar Haɗejiya aka fara gwama bukukuwan biyu lokaci guda.

### 4.1 Hawan Dawaki

A wannan binciken an fahimci cewa, baya ga wasannin al'adun gargajiya da ake gudanarwa a waɗannan ranaku. Babban abin da ya fi jan hankali a wannan buki, shi ne hawan dawakai da Sarakuna ke yi tare da hakimansu da dagatai da sauran jama'a mahaya dawaki. Wanda kusan wannan shi ne babban al'amari da ake gudanarwa a waɗannan masarautu. Kuma shi ne ke ƙara fito tare da bayyana dukkan al'adun Hausa a ciki. Domin kusan dukkan wata al'ada na ƙunshe ciki, da kuma dukkanin wasannin gargajiya da ake gudanarwa a ciki. Saboda haka, a waɗannan masarautu Sarakuna suna yin muhimman hawa guda uku, wato hawan ranar farko da hawan bariki/daushe da kuma hawan Magajiya/Mai babban ɗaki/Ɗantanoma. Wato sunan da ake kiran hawan ya danganta da masarauta, sai kuma ƙari a masarautar Haɗejiya da suke gabatar da hawa a rana ta huɗu wato hawan daushe na yara, wanda 'ya'ya da jikokin sarakai ke yi.

### 41.1 Rana ta farko

Kusan dukkanin masarautun da ke gudanar da bukin sallar gani, Sarki da sauran mahaya babu wani wuri na musamman da aka ware domin kai ziyara, sai dai kawai zagayen gari ta hanyoyin da aka ayyana ko aka saba bi. Wannan ta sa, hawan ba shi da wani takamaiman sunan da ake kiransa da shi, illa hawan ranar farko, ba kamar sauran ranakun ba. Saboda haka duk hakimin da ya fito da tawagarsa sukan je ƙofar fada (gidan sarki) ne a jira fitowarsa, daga nan sai a tafi zagayen gari kamar yadda aka saba. A Haɗejiya akan bi ta layukan da tsangayun malamai suke ne, da kuma gidajen manyan 'ya'yan Sarki (Mainawa). A sauran masarautun abun ba haka yake ba, ana gudanar da zagaye ne kurum.

### 4.1.2 Rana Ta Biyu

Bisa al'adar da ake gudanarwa a wannan rana a masarautar Daura da Haɗejiya ana zuwa bariki ne wato ofishin hukuma (inda Turawa suka zauna a lokacin da suke mulki). Ana gudanar da wannan hawa ne domin kai ziyarar gaisuwar ban-girma ga shugaban hukumar gwamnati a matsayin girmamawa. A da ana zuwa ofishin D.O (Turawan mulkin mallaka) ne, a yanzu kuma sai aka maye gurbinsa da shugaban ƙaramar hukuma da wakilcin babban jami'in gwamnatin jiha da makamantansu. Haka al'amarin kan kasance a masarautar Damagaram.

### 4.1.3 Rana Ta Uku

Wannan kuma ana kai ziyara ne ga wani muhimmin waje da aka tanada, domin kai ziyarar girmamawa ga mahaifiya ko 'ya'ya mata jinin saraki. Saboda haka a Daura ana kiran sa hawan Magajiya, a Haɗejiya kuma hawan ziyarar mai babban ɗaki. Yayin da Gumel ke kai ziyara zuwa gidan Sarki

Muhammadu Ɗantanoma (asalin wanda ya kafa garin Gumel), wannan ta sa ake kiran sa da hawan Ɗantanoma. A Damagaram ba su yin hawa a rana ta uku.

### 4.1.4 Rana Ta Huɗu

A masarautar Haaɗejiya ne kurum ake gudanar da hawan dawaki a rana ta huɗu, yayin da 'ya'ya da jikokin sarakai kan yi hawa cikin shiga irin ta iyayensu. Wato kowane ɗan hakimi da tawagarsa suna wakiltar gidansu. Haka kuma ɗan sarki shi ke shiga tare da fitowa irin ta mahaifinsa a matsayin Sarki. Wannan hawa ana kiransa da hawan daushe.

### 4.2 Tsarin Hawa

Hausawa suka ce, 'Girman asali, riƙe al'ada'. Da yake bukin sallar gani tamkar kwaikwayo ne na yadda al'ummar Hausa da sarakunanta suka kasance a baya, musamman lokacin yaƙi. Wannan ya sa ba haka kawai sarakunan kan gudanar da hawan dawaki ba, akwai dalilai da yadda ake tsarin hawan. Suna gudanar da hawan dawaki ne domin nuna al'adar Hausa ta amfani da dawaki wajen nuna ƙawa da yaƙi. Za a yi shigar yaƙi sanye da rigar saƙi da hamilu, da sulke da ƙwalƙwali da kuffi, a riƙe sanda ko takobi da mashi da garkuwa. Sannan a rataya kibiya da kwari da baka da makamantansu.

Saboda haka idan aka hau dawaki ana tafe ne cikin tsarin zuwa yaƙi. Tsarin kan zuwa ne sahu-sahu. Da farko hakimai ke zuwa a kan gaba, kusan kowa da matsayinsa, kuma su na tafiya ne bi-da-bi, wato girman sarauta da darajarta ko matsayinta. A farko akwai masu riƙe da sarautun jeka-na-yi-ka (title holders), sai kuma masu riƙe da ƙasa (district heads) sai 'ya'yan sarki masu riƙe da sarautar hakimta, 'yan majalissu na biye bayan su. Daga su kuma sai hakimai jarumai, kamar Sarkin yaƙi da Magayaƙi da Jarma da Garkuwa da sauransu. Sannan kuma sai tawagar Sarki, wanda 'yan tauri/masu dawa ke kan gaba, sai 'yan baka da maharba masu bindiga. Sai kuma 'yan lifidi da 'yan sulke biye a bayansu, sannan sai kuma kacakamu da dandalmu. Daga nan kuma sai dogarai mahaya dawaki da 'yan ƙafa. Sai kuma Sanƙira da zabiyoyi da zagage masu riƙe da sandar sarki su na layin tsakiya a gaban Sarki. Yayin da 'yan kakira masu riƙe da buta da kujera da darduma na gefen dama da haunin Sarki. Masu tambura da jauje da kakaki da algaitu da fare kuwa su na biye da Sarki a baya. Sannan kuma sai 'ya'ya da jikokin sarki suke biye da shi. A ƙarshen baya akan sami wani hakimi kamar Wambai a Haɗejiya ko Kaura a Daura, waɗanda kan kasance daga ƙarshen baya ne. Wannan yana nui ne da koda wani ya ji rauni ko an jefar da kayan yaƙi, su ke kula da su (majinyata ko kayan tsintuwa).

### 4.2.1 Dawakin Zage

Binckicen ya gano wasu dawaki da ake amfani da su a lokacin bukin babu mahayi, waɗanda ake kira da dawakin zage. Wannan wasu dawaki guda goma sha biyu ne, ana yi masu ado, a ja ragamarsu ba mahayi. Dalilin wannan dawaki shi ne, domin nuna irin yadda ake tafiya filin yaƙi, idan dokin wani jarumi ya kasa ko a ka kashe shi, sai a musanya masa da ɗaya daga cikin dawakin zage. A Daura kuma suna nuni ne da adadin sarauniyoyin da aka yi ne kafin Sarauniya Magajiya Daurama. Su waɗannan dawaki

ana jan ragamar su ne a gaban Sarki kafin zabiyoyi da zagage.

### 4.2.2 Amaryar Sarki

Bisa ga al'adar wannan buki na sallar gani, kusan a iya cewa a shi ne ake gwada duk wata al'ada da aka gada iyaye da kakkanni ta hanyar nuna ta a fili tamkar kwaikwayo. A yayin wannan hawa na gani akwai wasu dawakai guda biyu, waɗanda ake shirya su tsaf cikin ado, a lulluɓesu da babban bargo na alfarma, ana jan ragamar su ba mahayi, suna biye a bayan dokin sarki. Su waɗannan dawakai amfanin su shi ne, idan dokin Sarki ya gaza, ko ana da buƙatar sauya shi, sai a sauka a hau wani daga cikin amaryar sarki. Ana kiransa da wannan suna na amaryar sarki ne saboda lulluɓe shi da ake kuma a bayan dokin sarki a ke tafe da shi.

### 4.2.3 Tufafin Sarakai

Sarakai kan yi shiga irin ta sarauta, a sanya babbar riga aska tara ko tokarai ko tsamiya ko gwanda ko saƙiya ko 'yar yola ko ɗinke da makamantansu. Sannan a kan sanya alkyabba a kuma naɗe kai da rawani. Sarki da 'ya'yansa da duk wani wanda ya shafe shi yakan yi rawani da tsolo (kunnuwa) biyu, musamman a Daura da Gumel. Yayin da sauran hakimai da mahaya za su yi rawani da tsolo (kunne) ɗaya ko dungulumi.

A masarautun Daura da Gumel akwai sarautun mata, mata kan yi hawan dawaki kamar maza. Masarautar Daura akwai mata masu yawan gaske dake da sarautun ƙasar Hausa a yau. Sarautun mata sun ƙunshi irin su Magajiya da Garkuwa da Zinariya da Tambara da makamantansu. A Gumel akwai sarautar Magaram wanda ake naɗa babbar 'yar sarki. Saboda haka Magaram ta kan hau doki da tawagarta mata da maza, sanye cikin alkyabba ta rufe kai da ƙoƙuwa, wani lokaci kuma ta yi ɗaurin kallabin matan mutanen Borno. Haka su ma mabiyanta mata mahaya dawaki kan yi. Su kuwa mazan da ke biye da ita suna yin shiga ta yaƙi ne, su kuma tsaya a gefanninta dama da hauni. Makaɗa da maroƙa na biye da ita.

### 5.1 Sakamakon Bincike

A wannnan bincike an gano abubuwa kamar haka:

- Tasirin tsira da zama a ƙarƙashin tsohuwar daular Borno ta El-Kanemi ya haifar da samuwar bukin sallar gani a wasu masarautun ƙasar Hausa, musamman Haɗejiya da Gumel da Damagaram. Bisa la'akari da tarihin samuwar su, duk sun fito ne daga daular. Duk da cewa masarautar Daura an gano sun fi ba da ƙarfi wajen danganta samuwar bukin da al'adun da ake gudanarwa a ciki ga 'ya'ya da jikokin Bayajidda. Domin haka wannan ta sa ba kowace masarautar ƙasar Hausa ke gudanar da bukin ba.
- A lokacin bukin abun da ya fi jan hakalin al'umma shi ne, hawan dawaki da sarakai kan yi, domin irin shigar tufafi na gargajiyar Hausa da suke yi, da shiga irin ta yaƙi, da tafiya sahu-sahu tamkar za a yaƙi, sannan da tseren dawaki, domin tabbatar da asalin su a matsayin mayaƙa kuma jarumai.
- Akwai alaƙa mai ƙarfi tsakanin masarautun da ke gudanar da bukin sallar gani ta fuskoki da dama, kamar ta fuskar harshe da ƙabila da maƙwabtaka da auratayya da cinikayyar kayayyaki da sauransu.

Sannan an gano akwai nuna kara da girmama 'ya'ya mata da sarakai kan yi a wannan lokaci na bukin sallar gani, domin sarakai kan yi hawa domin kai ziyara ga 'yan uwansu mata musamman uwa da 'yan uwanta wato hawan Magajiya/mai babban ɗaki/ziyara.

- A ɓangaren wasannin gargajiyar Hausa kuwa, binciken ya gano ana gudanar da wasannin al'adun Hausa masu yawan gaske, kamar wasan bori da rawar taƙai da wasan wuta (babule/wowo) da na maƙera da wasan wanzamai da wasan manoma (yaro da garma) da wasan dambe da kokawa da shaɗi na Fulani da wasanni na ƙabilu daban-daban kamar Barebari da Yarbawa da Inyamurai da Tibi da Katafawa da sauran ƙananan ƙabilu mazauna Hausa. Sannan kuma ga wasanni da dabbobin gida da na daji, kamar Biri da Kura da Maciji da Kada da sauransu.
- Ta fuskar cinikayya, bincike ya gano ana samun yaɗuwar arziƙi da haɓakar tattalin arziƙi. Saboda akan sami baƙin 'yan kasuwa masu sayar da kayan dawaki da na mahaya da tufafi da takalman gargajiyar Hausa, da sauran masu baje kolin kayayyaki iri daban-daban. Yayin da 'yan gari musamman mata a gidajensu kan sayar da abinci da abin sha ga baƙi da 'yan gari da sauransu.
- Sannan kuma a bincike an gano, akwai sada zumunci a tsakanin sarakunan Hausa da maƙwabtansu, da shugabannin hukumomi da masu riƙe da madafun iko na ƙasa ko jiha da ƙaramar hukuma. Haka nan jama'a daga nesa kan ziyarci 'yan uwansu da ke cikin masarauta, waɗanda ke gari kuma kan sada zumunci zuwa ga 'yan uwansu na nesa. Domin akan kai ziyara zuwa gidajen 'yan uwa da abokan arziƙi, da ba da kyaututtuka ga manya da yara.
- Akan sami ƙulluwar hulɗa tsakanin baƙi da 'yan gari, da kuma maza da mata wanda hakan har yakan kai ga yin aure tsakanin saurayi da budurwa, wani lokaci kuma tsakanin zawarawa. Akasin haka kuma, akan sami saki idan saɓani ya auku, musamman ta dalilin al'adar nan ta wasu, mai nuni da ganin sarki ranar salla wankin ido ne. Idan miji bai amince da fitar masatarsa zuwa kallon salla ba, ta kan bijire wa umarninsa ta fita, wanda hakan kan kawo a sami saɓani har ta kai ga saki, aure ya rabu.
- Haka nan dai, binciken ya gano akwai ƙara ƙulluwar zumunci da samin haɗin kai da aminta da juna, tsakanin Hausawa da ƙabilun da ke zaune da su, musamman baƙin ƙabilu. Misali: ƙabilar Yarbawa da Inyamurai da Tibi da Katafawa da sauran ƙananan yaruka mazauna masarautun Hausa. Kusan dukkannin waɗannan ƙabilu suna ƙayatar da bukin sallar gani da yin wasannin gargajiyar al'adunsu, da shiga irin ta al'adarsu, da uwa-uba kuma hawa dawaki ranar hawa a matsayin sarakunan ƙabilunsu.

- A ɓangaren kiwon lafiya kuwa, an gano ta dalilin bukin sallar gani, baya ga sanya nishaɗi, zuciya ta nutsu da samin farin ciki, bukin yakan taimaka wajen gudanar da wasannin da kan sa jiki ya motsa, kamar wasan tseren dawaki, da wasannin yara maza (langa da boye da tsallake da guje-guje) da na mata (gaɗa) da makamantansu.
- Daga ƙarshe binciken ya gano cewa, da wuya a raba Hausawa da camfi, musamman masu sarautun gargajiya. Saboda haka binciken ya gano akwai wasu camfe-camfe da ake raɓawa da wannan buki na sallar gani. Misali: Idan saraki ya faɗo daga kan doki yayin kai jafi ga sarki, ana tsammata masa mutuwa kafin shekara ta zagayo. Ganin Sarki a kan doki, maganin ciwon ido ne. Yanka kaji domin bukin sallar gani, yana kawo wadata. Kyautar abinci a ranar farko ta bukin, yana kawo haɓakar arziƙi. Da sauransu da dama.

**Manazarta**


Ahmed, S. B. (1990) "Tsarin Sarautar Gargajiya a Haɗeja", kundin B.A, Kano: Jami'ar Bayero.

Bichi, A. Y. (2011) "Bayajidda Legend in the 21st Century: A Reassessment", in Yalwa, L. D. et al., (ed.) *Studies in Hausa Language, Literature and Culture*, Kano: Bayero University.

Bunza, A. M. (2019) "Sallar Gani a ƙasar Hausa Jiya da Yau": ƙasida da aka gabatar a Taron Karawa Juna Sani a Jami'ar Sule Lamiɗo da ke Kafin Hausa.

CNHN, (2006) *Kamusun Hausa*: Kano; Jami'ar Bayero.

Halima, K. D. (2015) "Hawan Magajiya A Masarautar Daura", Journal of Research In Arts And Social Science Education Vol.4 No. 1

Halima. K. D. (2016). "Kirarin Saraki a Bakin Mata: Nazarin Zabiyanci a Kasar Hausa", Kundin Ph.D, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Gaya, A. M. (1998) Tasirin Mulkin Gargajiya Jiya da Yau Musamman A Kano. Kundin Digiri Na Biyu; Kano: Jami'ar Bayero.

Gumel M. M (2019) "Sallar Gani A Garin Gumel A Kasidar Da Ya Gabatar A Taron Kara Wa Juna Sani A Jami'ar Sule Lamido Kafin Hausa

Ibrahim M.S. (1982) "Dangantakar Al'ada Da Addini": Tasirin Musulunci Kan Rayuwar Hausawa Ta Gargajiya: Kano. Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Bayero.

Kankara, I. S And Abubakar, A. (2018) The Place of Damagaram In The History of Daura: An Analysis of Contribution of Damagaram To The Development of Daura Emirate: Renaissance Culturelle Et Developpement Socio-Economique De La Region De Zinder, Du Nige Et De Lafrique. Colloque de l'Univesite De Zinder 10-11 December, 2018.

Koko, H. S. (2018) History and Cultural Ralations of Damagaram and Kanuri. Renaissance Culturelle Et Developpement Socio-Economique De La Region De Zinder, Du Nige

Et De Lafrique. Colloque de l'Univesite De Zinder 10-11 December, 2018.

Lange, D. (2012) The Bayajidda Legend And Hausa History; African Zion: Studies In Black Judaism. UK Cambridge Scholars Publishing

Maigatari, A. H. (2015) "Bikin Sallar Gani A Gumel". Kundin Digirin Babbar Difloma (PGDHS), Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Maimuna, L. D. (1987) "Fadar Daura", Kundin B.A, Kano: Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Nuruddeen, M. (1982) "Sallar Gani a Daura", Kundin Digiri Na Farko; Zaria: Sashen Hasunan Nijeriya da Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello.

Ramlatu, J. D. (2012) "Sarautun Kasar Daura da Muhimmancinsu ga Al'umma" Cikin *Champion of Hausa Cikin Hausa*, Amfani, A.H. da Wasu (ed) Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Sarkin Tarihin Daura (2019) "Asalin Sallar Gani a Kasar Hausa Jiya da Yau. A Taron Kara wa Juna Sani: Jami'ar Sule Lamiɗo Kafin Hausa.

Saulawa, A. M. (2001) "Origin of the Hausa States Revisited" in *Degel Journal, Faculty of Arts and Islamic Studies*, Sokoto: Usmanu, Ɗanfodiyo University.

Shafa'atu, M. T. (2013) "Kirarin Mata a Kasar Sakkwato", Kundin M.A, Sokoto: Jami'ar Usmanu Danfodiyo.

Smith, M. G. (1978) *The Affairs of Daura*,__London: University of Califonia Press.

Tsiga, I. A. (1978) "Sarauniya Daurama", Takarda, Taron Kungiyar Hausa, Kano: Jami'ar Bayero. r Bayero.

Wakili, H. (2005) *Turawa a Kasar Hadeja*, Kano: Benchmark Publishers Limited.

**Wasu Da Aka Yi Hira Da Su**

| Lamba | Suna | Shekaara | Ranar da aka yi hira | Adireshi |
|---|---|---|---|---|
| 1. | Alhaji Muhammadu Chilchili Dogon direba Gumel | 96 | 16/08/2025 | Unguwar Zuwo, bayan gidan Sarki Gumel |
| 2. | Baba Garba Mai Fata | 67 | 09/08/2025 | Unguwar Kasuwar Kuda Haɗejiya |
| 3. | Alhaji Sani Takarace | 87 | 12/06/2025 | Unguwar Kasuwar Kuda, Haɗejiya |
| 4. | Hajiya Nafi Idris | 64 | 30/07/2025 | Unguwar Zuwo, bayan gidan Sarki, Gumel |
| 5. | Alhaji Hamza Sarkin Baƙin Daura | 78 | 21/08/2025 | Fadar Daura |
| 6. | Wakilin Tarihin Daura | 64 | 21/08/2025 | Fadar Daura |